

DEREK PRINCE
MINISTRIES INTERNATIONAL

Abincin Yini

Rayuwar Ruhaniya: Zumunci da Allah

Yesu ya mutu domin ya sada mu da Allah har abada



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Bayan Bitrus ya zare takobinsa don ya kare Yesu, saboda kada a kama shi a lambun Getsamani, Yesu ya ce masa:

> "Maida takobinka kube. Ba sai in sha ƙoƙon da Uba ya ba ni in sha ba?" (Yahaya 18:11)

Yesu ya shanye ƙoƙon har da dago-dagon. Ka gani, aikin Yesu bai kare a kan gicciye ba. A gaskiya, ainihin dago-dagon wahalar ta zo ne bayan mutuwar jiki. Ta kowace fuska, Yesu ya shanye ƙoƙon. Da farko, akwai mutuwar ruhaniya; na biyu, mutuwar jiki; na uku kuma, yashewar Allah ta ruhaniya.

Yesu ya ɗanɗana mutuwa saboda kowanne mutum domin mu sami rai. Kuma mun sami rai ta ɓangarorin rayuwa guda uku da Yesu ya rasa su. Komai ya tafi daidai.

Da farko dai, muna da rayuwa ta ruhaniya—an kawo mu cikin ɗayantuwar zumunci da Allah a cikin wannan rayuwar, yanzu haka, ta wurin bangaskiya ga Yesu Kristi. A haɗe Yesu yake da Ubangiji; Ya rayu ta wurin rayuwar Uba. Ya ce, "Ni da Ubana ɗaya muke" (Yahaya 10:30). Haka abin yake har zuwa lokacin da Ya ɗauki zunubanmu a kansa sannan Ya rabu da Uba. Ya mutu domin mu sami ɗayantuwa. Ta wurin bangaskiya ga Yesu, ni da kai za mu iya haɗuwa da Ubangiji cikin Ruhu mu yi wannan rayuwa cikin ɗayantuwa da Allah, kamar yadda Yesu ya yi rayuwar ɗayantuwa da Uba ta wurin Ruhu. Wannan ita ce manufar ƙarshe ta bishara.

Yahaya ta fari 1:3 ta ce:

> "To, shi wannan da muka ji, muka kuma gani, shi ne dai muke sanar da ku, domin ku ma ku yi tarayya da mu; haƙiƙa kuwa tarayyar nan tamu da Uba ne, da kuma Ɗansa Yesu Kristi"

Yesu ya rasa zumuncin domin in shiga cikin zumuncin.

Na gode maka, Yesu, saboda aikinka a kan gicciye. Ina furta cewa Yesu ya ɗanɗana mutuwa domin in sami rai; ya mutu domin in sami ɗayantuwa; ya rasa zumunci domin mu shiga

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

cikin zumuncin. Ina furta cewa Yesu ya mutu domin in sami ɗayantuwa da Allah har abada. Amin.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-148-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.